**Competitive Scramble is an Evil Ingenuity: Proceedings from the International Conference on the Biography and Songs of Alhaji Abubakar Kassu Zurmi in Heroic Poetry**

**A Publication of the Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto**



| ISBN 978-978-62480-5-9 (Print) | ISBN 978-978-62480-5-9 (Online)

**DOI:** https://doi.org/10.65760/kassu.i1.28 **Website:** www.ssu.edu.ng |Issue 1 | April 2025|

# Mawaƙi Ɗaya Muryoyi Goma: Nazarin Kwaikwayon Muryoyi A Wasu Waƙoƙin Kassu Zurmi

**Nasara Bello Dogon Daji**
Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Jihar, Sakkwato

**Corresponding Author: Nasara Bello Dogon Daji** nasarabdogondaji@gmail.com
GSM: +2340860553367

**Tsakure**
Mawaƙa na da hanyoyi iri-iri fa suke bi wajen aiwatar da waƙoƙinsu da kuma amfani da salailai nau'i-nau'i domin sanya armashi. Wannan maƙala mai suna, "**Mawaƙi Ɗaya Muryoyi Goma: Nazarin Kwaikwayon Muryoyi a Wasu Waƙoƙin Kassu Zurmi"** maƙala ce da ta yi nazarin ɗaya daga cikin hikimomin da waƙoƙin Kassu Zurmi suka ƙunsa wato kwaikwayon muryoyi daban-daban na mutane da ma wasu sauran halittu. Maƙalar ta yi amfani da waƙoƙi kamar *waƙar Nomau Namagarya* da *waƙar Shayi Ɗangidan Labbo* da *waƙar Muhammadu Fatake na Dare* haka kuma ana iya lalubo misalai daga wasu waƙoƙi masu salo makamancin na Kassu Zurmi. Manufar wannan maƙala ita ce a dubi irin hikimar Kassu wajen kwaikwayo a cikin waƙarsa, sannan a dubi shi kansa kwaikwayon yadda ya rarraba da kuma yadda ya yi amfani da su a cikin waƙoƙinsa. Bincike maƙala dai ta jingina ne falsafar waƙe Magana ta Hausawa da ke cewa « Kai kaɗai gayya" da ma dai Kassu Zurmi ba karɓi ake masa ba, saboda haka duk hira da tattaunawar da ka ji cikin waƙoƙinsa duk shi kaɗai ne ke hidimar sa. Abin da binciken wannan maƙala ya gano shi Kassu Zurmi ya yi amfani da dabarar mawaƙa ta amfani dabarar kwaikwayon mutane har ma da amfani da adon harshe da wasu masana suka kira jinsarwa wasu kuma suka kira shi jinsantarwa. Mawaƙin ya jinsantar da tsuntsaye da karkuna.

**Copyright:** *Provided that the author(s) and the source are credited, noncommercial use of the article is allowed, including printing and distribution.*

## 1.0 Gabatarwa

Mawaƙan baka a cikin al'umma ba ƙaramin matsayi gare su ba, musamman idan an yi la'akari da irin gudunmawar da suke bayarwa wajen zama wata taska ta adana muhimman bayanai na tarihi ga al'umma. Sannan ga irin rawar da suke takawa wajen yekuwar shirye-shiryen gwammati da sauran hukumomi da jam'iyyun siyasa da 'yan

siyasa, sannan uwa uba nishaɗantar da al'umma. Makaɗa Kassu Zurmi a matsayin sa na ɗaya daga cikin mawaƙan Hausa, ya yi irin nasa waƙoƙi a duniyar mawaƙan maza.

Duk da yake Kassu Zurmi yana kwaikwayon muryoyi mutane, har da tsuntsaye da dabbobi, mun san cewa akwai sauran mawaƙa masu irin wannan salon kamar Sa'idu Faru wanda a cikin waƙarsa ta 'Sarkin kudu' da Mamman Gawo Filinge a waƙar sa ta 'Ya Allah gyara Wahabu ka Taimaki 'Yannijar' Haka shi ma Ɗanammani Maikuntugi Wurno, cikin waƙar sa ta Ilaje Maibaka Danmamman shi ma ya yi amfani ya yi amfani da kwaikwayon muryar tsuntsuwa.. Abin lura dai a wannan shimfiɗa shi ne, duk waɗannan mawaƙan sun yi tarayya da Kassu Zurmi wajen amfani da dabarar kwaikwayo.

Sai dai abubuwan da suka sa Kassu Zurmi ya ƙara yin fice a waƙoƙinsa su ne irin yadda yake sa hikima da dabarun salailai iri -iri a cikin akasarin waƙoƙin sa musamman amfani da kwaikwayo. Kafin a zurfafa cikin maƙala akwai buƙatar a waiwayi tarihin makaɗin a taƙaice.

## 2.0 Taƙaitaccen Tarihin Kassu Zurmi

Kassu Zurmi an haife shi a garin Magarya ne, kimanin kilomita ashirin da huɗu (24) zuwa garin Zurmi, Zurmi ƙaramar hukuma ce a jihar Zamfara. Bayan Kassu Zurmi ya tasa ya zama matashi, sai ya koma garin Kadawa misalin kilomita biyu (2) zuwa garin Magarya wato mahaifarsa.

### 2.1 Kuruciyarsa da Ilminsa

Kamar yadda ya gabata, Kassu wanda sanannen sunansa Abubakar da ya tasa ya koma Kadawa ya haɗu da sauran matasa tsararsa. Ya kasance hatsabibin gaske marar tsoro a cikin abokansa. Haka kuma, saboda irin ƙiriniyarsa da taƙadarcinsa ya kasance mai kwarjini ba tsakanin abokansa ko tsararsa kawai ba har ma da manyan mutane. Kassu Zurmi bai samu yin karatun zamani ba amma ya yi na Muhammadiyya a wajen wani malaminsa Malam Ladan kuma ya samu har ya sauke Alƙur'ani a wajensa har ya fara littattafan ilmi, sai dai bai yi zurfi ba sai lamarin kiɗa ya ɗauke hankalinsa ya ci gaba da kiɗansa (Gusau, 2005:225).

### 2.2 Fara Waƙarsa

Kassu Zurmi dai ya gaji kiɗa ga mahaifinsa. Mahaifinsa makaɗin fawa ne kuma yana kiɗan bori, daga bisani ya dawo yana kiɗan farauta kuma daga nan ne Kassu Zurmi ya fara koyon waƙar farauta. Saboda haka, Kassu gadon kiɗansa ya yi ba haye ya yi ba daga sama.

### 2.3 Yaran Kassu Zurmi da Nau'o'in Waƙoƙinsa

Kassu Zurmi yana da 'ya'ya biyar kamar haka:

i. Dodo
ii. Tunau
iii. Shata
iv. Namalka
v. Umaru Ƙaho

Nau'o'in Waƙoƙinsa sun haɗa da:

i. Kiɗan Noma
ii. Kiɗan Farauta
iii. Kiɗan 'Yan caca
iv. Kiɗan Ɓarayi
v. Kiɗan Fawa (Gusau, 2005:229).

Kassu Zurmi ya yi aure yana da 'ya'ya da dama. Cikin 'ya'yansa akwai Umaru wanda shi ne makaɗin tauri, wato wanda ya gaje shi. Sauran akwai Usman wanda ya bi hanyar karatun addini kuma shi malami ne yana koyarwa. Akwai Kuma 'Yarjari da Auta da Abu da Karɓa, Kassu dai na da 'ya'ya sun kai goma sha biyu (12). Makaɗa Kassu Zurmi ya rasu a shekarar 1987 a asibitin Gwaji na Gusau bayan 'yar gajeruwar rashin lafiya.

### 3.0 Mawaƙi Ɗaya Muryoyi Goma

Makaɗa Kassu Zurmi, makaɗi ne da za a iya yi wa kirari da "Kai Kaɗai Gayya" domin mutum ɗaya ne tamkar goma idan yana cikin aikinsa na waƙa. Domin yakan yi kwaikwayo na zahiri[1]. Sannan ya yi kwaikwayo na zantuttukan mutum ɗaya ko biyu ko fiye da haka. Misali dattawan da suka kira Kassu cikin zaure domin a yi baikon Shayi ai ba a san addininsu ba. Haka su ma 'yammatan da suka yi ta ribibin Shayi saboda su jiɗar da shi su ma ba a san ko su nawa ba ne. Shi ya sa maƙala ta ce, "Muryoyi goma". Salailan da makaɗa Kassu ya yi amfani da su sun kasu gida huɗu dangane da waƙoƙin da aka zaɓa kamar haka:

i. Kwaikwayon muryar mutum ɗaya
ii. Kwaikwayon muryoyin mutane da yawa
iii. Kwaikwayon muryoyin dabbobi
iv. Kwaikwayon muryoyin tsuntsaye

### 4.1 Salon Kwaikwayon Muryar Mutum Ɗaya

Wannan hikima ce ta Kassu Zurmi inda a cikin yawancin waƙoƙin sa ya yi amfani da shi, inda za ka ji Kassu yana tattaunawa ko hira da wani. Idan muka shiga cikin waƙar "Nomau na Magarya" ta Kassu Zurmi inda aka gayyaci Kassu domin ya karɓi dokin Nomau a (Gusau, 2009:365).

Doki da gamgami sai Nomau na Magarya
Ubanbalindo shi ya ishe ni hak Kadawa
Yac ce *Kassu ana biɗak ka da doki*
*Ga ka kana Alhwarma*.
(Kassu Zurmi, Waƙar Nomau)

A nan Kassu ya kwaikwayi managar Ubanbalindo na saƙon albishir na doki kuma za su fara tattaunawa, ya yi muryar Ubanbalindo cikin rubutu mai tafiyar tsutsa saura ta shi.

Ɗankalgo bani ƙaunar ƙarya,
Wa ka sai mani doki Magarya?
Nomau na ko abin tuwo ba ya da shi,
Kahiri Karen Bunun Baƙo,
Yanzu kau Karen Alhaji ne.
(Kassu Zurmi, Waƙar Nomau Namagarya)

Wannan shi ne martanin Kassu ga mai saƙo. Idan muka shiga cikin wannan waƙar, akwai inda Kassu ya kwaikwayi muryar Nomau, bayan ya ba da shawarar wada za a yi a samu doki :

Bari sai gobe da swahe
Iskan nan ya taso
Wanga na shi ƙag gajiya

[1] Idan akwatin talabijin ko bidiyo ka kallon waƙar Shayi Ɗan gidan Labbo, za ka ga yadda yake koyon rawar Tantabarin Shayi lokacin da yake yi wa Shayi waƙa kafin ya watsa mai tsaba da kuma yadda karkuka ke habshi idan idan sun ga ɓarayi. Sanna ɗaya daga cikin dattijawan suka zo baikon Shayi, shi ma Kassu ya koyi yadda ya buge rigar sa ya fita zaure da ya ji cewa Shayi bai iya ciyar da matarsa.

Mai kwasas Sansami ya na gamawa da ƙasa
Ya baf faƙo kar-kar-kar
Sannan ebo wuta ga ragga ko hito
Koma da zuwa gidan Ɗan Aljanna
Hwalka ‘yab bura uba sai daji
Na Magaji rantsuwa ka ta kasau
Gama da ‘yan kashin wuta za ni hita
Yacce Kassu *shawarakka ita za ni biya*
Baba in kau kab bi ta
Gobe dokin aka yi
Magarya ko ba su da shi.
(Kassu Zurmi, Waƙar Nomau Namagarya)

Idan mun lura layi mai rubutun tsutsa shi ne kwaikwayon muryar Nomau ce. Kassu Zurmi kai kaɗai gayya duk zancen shi kaɗai ke yi.

**4.2 Salon Kwaikwayon Muryar Mutane da Yawa**

Bayan inda Kassu ke kwaikwayon mutum ɗaya, akwai kuma inda Kassu ya shiga muryar jama’ar da ba a iya gane adadinsu. Misali a cikin (Gusau, 2025 :365-368) lokacin da suka je wasa a Magarya, ‘yammata sun tafi tarbon baƙi kusa da gebe, kuma ga abin da makaɗa Kassu ke cewa:

Wasan da mun ka zo
Tare da ‘yan Magarya tai kyawo,
Rannan Sha yaya yas shigo sa’a
Ga ya da dogon baƙi da yaw wutaɓ ɓota
Na Abu yankan bakinka ya yi ma kyawo
Ya samu gama aron zanen saƙi
Had da tsamiya yaɗ ɗauro da yab bakas shadda
(Kassu Zurmi, Waƙar Shayi Ɗangidan Labbo)

Kassu ya ba da bayanin irin wankan Shayi da kuma yadda ya ɗauki hankalin ‘yammatan Magarya, kuma mun ga inda Kassu ya kwaikwayi muryar ‘yammatan cikin faɗa a kan Shayi (Gusau, 2009:367).

Sun gane shi sun je mai,
An ka ɗora wasoso,
*Ni wan’in Shayi ni ka jide shi*
*A’a kina ƙarya na riga ki zaɓo shi*,
Kamas su buga ga su nan cikin gebe,
Na ce kak ku buga ya ishe ki jiɗawwa.
(Kassu Zurmi, Waƙar Shayi)

Layuka masu tafiyar tsutsa na nuna muryoyin ‘yammata da Kassu ya kwaikwaya, kuma ko su kasance su biyu ne kokuma ba a san adadinsu ba, ya shiga tsakaninsu domin hana rigimar kan Shayi. Wani kwaikwayo mai kama da wannan shi ne na gaba wato shi ne bayan wasa ta ƙare za a watsewa. Iyayen ‘yammata suka jawo Kassu.

Sai da zamu watcikkewa
Kana uwayen matan ga sun ka jawo ni,
Ga ni ga ‘yan matanga ga uwayensu,
Mu kaɗai cikin zaure,

*Kassu amana Allah ka ba mu labari,*
Nic ce wane labara,
*Labarin Shayi ɗan gidan Labbo,*
*'Yam mata sun walwale baikonsu,*
*Sun ce Shayaya shi ka rankonsu*
*Shi muka son ka ba mu labari,*
*In akwai gidan kirki.* (Gusau, 2009:368).
(Kassu Zurmi, Waƙar Shayi)

A nan Kassu ya yi kwaikwayon muryoyin dattawa iyayen 'yam mata.Kuma ba a san adadin yawan dattawan ba saboda mutun ɗaya ya yi Magana da Kassu a mudadin saura. Idan muka duba tun daga layi na biyar (5) har zuwa layi na goma sha ɗaya (11) duk kwaikwayon muryoyin iyayen 'yammata ne ya kwaikwaya, layuka masu tafiyar tsutsa.

**4.3 Salon Kwaikwayon Muryoyin Dabbobi**

Kassu kai kaɗai gayya ya tsallaka har cikin duniyar dabbobi ya nuna hikimarsa ta kwaikwayon habshin Kare. A waƙar Muhammdu Fatake na Dare, Kassu Zurmi yana ishara ga masu Karnuka da su kiyaye nau'in habshin Karnukansu:

Abin da ba mu so dandokar dare
Kun san ɗan dokad dare taro?
A'a Shegen ƙwaran ga
Mai ɗangatan uwas sauri karen gida
Bai aje ba, bai bai ba wani ajiya ba
Sai yay yi tsugunne
Ya hana ido nai kwana
Habshin mutum daban da na kura
In kaj ji Karenka ya kwashi habshi
Ya yi bakin gida
Ya dawo dab baya-baya
Ya ɗora bugun ƙofaɗ ɗakinka
Kura ce
Gudummuwa ka cetai an nan
Amma habshin ɓarai
Idan an kwasa an tai bakin gida
An ka kewayo hina
Gasu gasu gasu gasu gasu
Gasu gasu gasu gasu gasu gasu

To kar ka saki ku hito masu yi sun kawo.
(Kassu Zurmi, Waƙar Muhammadu Fatake na Dare)

Kai kaɗai gayya Kassu Zurmi ya yi amfani salon jinsintarwa domin gashi ya sa kare yana magana kamar mutum ya kwaikwayon habshin kare ta hanyar amfani kalmin ishara.

**4.4 Salon Kwaikwayon Muryoyin Tsuntsaye**

Kassu Zurmi ya shiga duniyar tsuntsaye wajen bayyana hikimarsa ta salo. Idan an koma ga waƙar Shayi musamman tsakaninsa da tantabarinsa. Mai yi masa mabanci da safe. A (Gusau, 2009:367) Makaɗa Kassu na bayani :

"Tantabari na rigan ka tasowa
Sai tsuntsu yah hito yana shan hanci

Yana kashin ƙeyya
Shina dubin inda za ka hudowa
Shi kau yana cikin ɗaki”
(Kassu Zurmi: Waƙar Shayi)

Tantabari na gyaran jiki nai
Sai da Sha yaya yaɗ ɗago ɗaki
*Ɗam mazan tantabarin ga na yi mai guɗa*
*Shina Kundunguru Shayi ɗan gidan Labbo*
Shi ko Koƙirzon sai ya watsa ‘yat tsaba
Kai ko tsuntsu tcince tciyakku ta bi ku
(Kassu Zurmi, Waƙar Shayi)

Idan muka duba layi na uku da huɗu masu tafiyar tsutsa sun ɗauki irin kwaikwayon da Kassu ya yi na kukan tantabari amma a nan Kassu ya sake yin amfani da salon jinsintarwa (Gusau, 2003:59) abin da (Yahaya, 2001 :79-89) ya kira dabarar jinsarwa, saboda makaɗa Kassu ya ba tantabari sifa ta aiki irin na jinsin mutum har yana yi wa maigidansa ma’abbanci.

Har yanzu dai a duniyar tsuntsaye muna kan waƙar Shayi wato tsakaninsa da kurciyar gamji lokacin shuka:

”Shi na sari nan ana yi mai shikka
Sai ya tcinkayi kurciyag gamji
Can tana ta ƙotonta
Na Abu ya biɗo dutci
Nan inda yad duƙa tsuntsuwagga tat tashi
Ya tashi ya diba
Ya diba bai ga inda ta hau ba
Ashe ko tsuntsayen daji na da azanci
Sai ya yadda dutci
Ya wuce bisa dutci ya sari gargare ukku
*Bari dai mu yi mai magana*
*Kahin dai ya gane dutcin can*
*Na gane shi na tashi*
Shi na sara wa ta na yi mai launi
*Ko gwallo ko gwallo*
*Ko gwallo ko gwallo ko gwallo*
*Ko gwallo* in ji Kurciyag gamji”

Nan ma Kassu Zurmi ya yi amfani da salon jinsarwa da ya yi wa Kurciyar gamji kwaikwayo. Salon da ya yi amfani da shi wajen kwaikwayon tantabari shi ne ya yi amfani da shi ga kurciyar gamji. Duk layukkan da ke cikin tafiyar tsutsa kalaman kurciyar gamji ce Kassu ke koyo

## 5.0 Kammalawa

Wannan maƙala ta gano cewa Abubakar Kassu Zurmi ɗaya daga cikin jerin mawaƙan maza na Hausa yana da hikimomi da dama waɗanda Allah ya yi masa baiwar su, sai dai maƙala ta dubi dabarar da ya faye amfani da ita a yawancin waƙoƙinsa wato kwaikwayon muryoyi amma manazarta ba su kula da yin tsokaci a kai ba. Wato irin yadda Kassu Zurmi

ya shahara ga kwaikwayon a cikin waƙoƙinsa, idan ya shiga fagen kwaikwayo mai saura zai yi tunanin da 'yankarɓi masu yawa yake waƙa. Sannan Kassu sai ya zama ruwan zafi ba kada gefe, yadda zaka ji kwaikwayon sa a waƙar tauri ko farauta haka zaka ɗuriyar kwaikwayon a waƙar noma ko ta ɓarayi. Kuma wannan na daga cikin abubuwan da suka sa armashin da karɓuwa ga waƙoƙinsa.

**Manazarta**


Abdulƙadir, D. (1979). *Zaɓaɓɓun waƙoƙin da da na Yanzu*. London, Thomas Nelson (Nigeria) Limited.

Gusau, S.M. (1993). *Jagoran Nazarin Waƙar Baka*. Kano Benchmark Publishing Limited.

Gusau, S.M. (2008). *Waƙoƙi A Kasar Hausa, Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu*.

Gusau, S.M. (2009). *Diwanin Waƙoƙin Baka : Zaɓaɓɓun Matanoni na Waƙoƙin Baka na Hausa*. Kano : Century Research and Publishing Limited.

Gusau, S.M. (2018). *Diwanin Waƙoƙin Baka Juzu'i* na Uku, Kano: Century Research and Publishing Limited.

Jami'ar Bayero, (2006). *Kamusun Hausa*. Kano, Cibiyar Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

Magaji, A. (2016). *Kassu Zurmi da Waƙoƙinsa*. Ibadan: Spectrum Books Limited.

Sayaya, A.S. (2009). 'Wasar Tauri a Kasar Katsina'. Kundin Digiri na Biyu da aka gabatar a Sashen Harsunan Nijeriya. Sakkwato : Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo.

Umar, M.B. (1980). *Adabin Baka*, Zaria, Northern Nigeria Publishing Company.

Yahya, A.B. (1997) *Jigon Nazarin Waƙa* Kaduna Fisbas, Media Service

Yahya, A.B. (2001) *Salo Asirin Waƙa* Kaduna Fisbas, Media Service

Yahaya, I. Y. (1988). *Hausa A Rubuce: Tarihin Rubuce-Rubucen Hausa.* Zaria: Northern Nigeria Publishing Company.

Yahaya, I. Y. & Danganbo, A. 1986. *Jagoran Nazarin Hausa*. Zariya: NNPC

Okeke V .O.S.K2013ƙ: "Community Policing, Vigilante Security Apparatus and Security Challenge in Nigeria: A Lesson From Brain and Igbo Traditional Security in Nigeria"